# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Ni ma ɗan Adam ne: 'Yan Afirkan da ke fama da taɓin hankali
## Kashi na huɗu: Hali mai kyau da marasa kyau

Wanda ya rubuta: Chrispin Mwakideu
Wanda ya fassara: Yusuf Idris
Wadda ta tace: Halima C. Schmaling

**'Yan Wasa:**

Mutum: ɗan shekara 45
John: ɗan shekara 25
Jane: 'yar shekara 25
Fasto: ɗan shekara 40
Amina: 'yar shekara 19
Mai gadi: ɗan shekara 30
Duduwa: 'yar shekara 35
Musa: ɗan shekara 16

**Mai gabatarwa:**

Masu sauraronmu, barkanmu da sake kasancewa da ku a cikin kashi na huɗu na shirinmu na "Ji Ka Karu" wanda muke kawo muku a kan mutane masu taɓin hankali a ƙasashenmu na nahiyar Afirka. A cikin shirin da ya gabata kun ji yadda Duduwa ta kai ɗanta Musa wajen wani mai maganin gargajiya, wato Maude, bayan an kore su daga asibiti inda ta kai shi domin nema masa magani, wai saboda yana da taɓin hankali. Ita kuma Amina ta je ta ga wani likitan ƙwaƙwalwa Dr. Mudi, wanda ya shawarce ta da ta riƙa zuwa yana duba ta a kai-a kai.

To yau me shirin yake ɗauke da shi? Taken shirin na yau shi ne: "Hali mai kyau da marasa kyau". Za mu faro ne daga ƙauyen su Duduwa, inda da sassafe maƙwabtanta suka zo suka zagaye ɗan ƙaramin gidanta na jinka.

**Fitowa ta 1: A gidan Duduwa**

**Mutum:** Duduwa! Yau ƙaryarki ta ƙare! Mun gaji da maitar da ki ke yi mana. Duduwa, ki fito na ce, ko kuma mu sa wa wannan jinkan naki wuta! Kina jinmu? Ba ma so mu riƙa zama da mayu a cikinmu! Lokacinki ya cika. ... Wannan shi ne damarki ta ƙarshe. Idan ba ki fito ba za mu sa wa wannan wurin wuta. Shi ke nan, ta ɗauka wasa muke yi, ba ni kwalin ashanan nan. ... Muna fata da ke da maitarki ku ƙone a cikin wutar nan! Nan ƙauyen ba wurin zamanki ba ne, har ɗanki ma kin ba da shi ga mayu kuma kin jawo wa wannan ƙauyen namu bala'i. Ba ma samun ruwan sama, dabbobinmu sai mutuwa suke ta yi, sannan jama'armu ma na ta kamuwa da cuta. Muna yin abin da muke yi ne don mu kori shaiɗanu daga ƙasarmu! ... Jama'a ku gudu, in ba haka ba aljanu za su kubce su shige ku.

**Mai ba da labari:**

Gidan jinkan nan na Duduwa sai ya kama da wuta nan take! Kuma ba da wani ɓata lokaci ba ya ƙone ƙurmus. Shin maƙwabtan nan sun yi daidai kuwa a kan abin da suka aikata? Saboda kawai suna zargin cewa Duduwa mayya ce? Wai don kawai akwai wani mai taɓin hankali a cikin iyalinka sai a mai da kai maye?

Amma yanzu bari mu koma wurin John. Bayan ya rasa aikinshi sai ya daina sha'awar komai. Maganar gaskiya ma ita ce, yanzu yana fama ne da ciwon takaici. Amma da shi da matarshi Jane ba su fahimci haka ba. To sai Jane ta kawo wani wanda take ganin zai iya taimaka masa.

**Fitowa ta 2: A gidan John**

**John:** Sakarai, shashasha, maras amfani! Abin da na zama ke nan. Ni ba mijin ƙwarai ba ne, ni ba abokin zama na ƙwarai ba ne, ni ba abokin ƙwarai ba ne, ballantana maƙwabcin ƙwarai! To ta yaya za a yi in zama uban ƙwarai? Ba zai yiwu ba. Meye amfanin rayuwa idan ba za ka zama abin da kake so ka zama ba, idan ba za ka samu abin da kake so ba? ... Na daure wa wannan abin kunyar. Ba zan bari ɗana da za a haifa ya gan ni ba. Na ba ɗan ma kunya tun kafin a haife shi. Na zama abin kunya ga iyalina da zuru'ata da jama'ata. Shi ke nan, ya kamata in rubuta wasiƙar nan da wuri kafin Jane ta dawo daga coci.

Zuwa ga Jane, matata abin ƙaunata. Ki yi haƙuri da irin halin takaicin da zan jawo miki, amma na yanke shawarar in ɗauki raina saboda na riga na daɗe da mutuwa. Don Allah kar ki yi kuka. Ki kula da ɗanmu idan kin haihu. Ki yi haƙuri.

Na ƙi jinin duniyar nan! Da ma na ƙi jinin aikin da nake yi! Wannan shirmen ya isa haka! Lokaci ya yi da zan fuskanci matsalata. ... Arrrgh!! Ahhh, kaina na zafi. Ba zan iya ci

gaba da zama haka ba. Jane ba ta san yadda nake ji ba. Ba wanda ya sani, ba wanda ya damu. Duniyar nan ba ta da tausayi. … Mama da Baba, na kusa zuwa in same ku a inda kuke hutawa, cikin ramin nan. Wataƙila zan samu kwanciyar hankali daga wannan bala'in da ke damuna. ...Ku ƙyale ni! Ina so in mutu cikin kwanciyar hankali. Ku tafi! Ku ƙyale ni!

**Jane:** John! Ni ce, maigidana. Na dawo, kuma na zo da wani daga coci. Ka buɗe mana kofa. Ban ga makullina ba.

**John:** Jane, ki yi haƙuri. Na rubuta komai da komai. Komai zai tafi daidai. Za ki gani.

**Jane:** Fasto, ka ga abin da nake nufi ko? Ka ga abin da nake gaya maka ko. Ba John ɗin da na sani ba ne. Me yake nufi da cewa ya rubuta komai da komai?

**Fasto:** Yi sauri, ki buɗe mini ƙofar nan! Ina ganin ma ƙoƙarin kashe kanshi yake yi ne!

**Jane:** Wayyo Allahna! Ina! Kai! Haka ba zai yiwu ba. Ina makullina?

**Fasto:** Ba mu da lokaci fa! Ina ganin kawai zan ɓalle ƙofar nan. ... John! John, kana ina ne? Ina kake ne, John?

**Jane:** Ga shi, ga shi! Ga shi ya zauna kusa da kabat. Ga shi nan.

**Fasto:** John, don Allah kar ka sha wannan abin. Na zo ne in yi maka addu'a. Matarka ta faɗa min komai da yake faruwa.

**Jane:** Oh... huuu! Zan haihu! Zai fito. Wash! Aaa...

**Fasto:** Mene!? Yanzu? To shi ke nan. To ta ina ma zan fara ne? Ga wannan ba lafiya, ga wannan kuma.

**Jane:** Aaaah… John… ka tashi! Zan haihu. John!

**Fasto:** Kwarai! John, matarka tana buƙatar taimakonka, ɗanku yana buƙatar uba. Kar ka yi musu haka.

**John:** Jane matata! Ba wani abin da ya same ki dai ko? Ikon Allah. Lokaci ya yi! Ina nake ne? Shi ke nan. Fasto, mu yi sauri mu kai ta asibiti. Ka zo da motarka ne?

**Fasto:** Ba damuwa John. Amma ba ka ganin ya kamata ka ɗan yi wanka ka canza kaya? Idan mutane suka gan ka a cikin wannan yanayin da kake za su yi tunanin ka ɗauki makwanni ba ka yi wanka ba.

**John:** Fasto, mu tafi kawai. Mu tafi!

**Fasto:** To shi ke nan, mu tafi!

**Jane:** Wash! Aaah... fuuuu... Don Allah ku yi sauri! …

**Mai ba da labari:**
Don da ba a riga an haifa ɗa ba dai ya ƙwaci mahaifinshi John. Amma ba kowaɗane mutane ba ne da suka shiga cikin hali na takaici ke samun irin wannan damar.
A yayin da suke tafiya zuwa asibitin, su kuma ɗaliban makarantar koyon aikin nas sun fito hutun rabin lokaci. Amma Amina ba ta tare da su. Ba ta sake komawa don ta ga Dr. Mudi ba, kuma halin da take ciki ya ƙara ƙazanta. Ta gudu daga makaranta, kuma tana ta gararanba a kan titi, tana ta yawo tana

Magana ita kaɗai da kuma masu wucewa. Amma ba mai gane abin da take faɗi.

**Fitowa ta 3: A hanya**

**Amina:** Hehehe! Ni ce likita, kai kuma kai ne maras lafiya! Kai! E, da kai nake! Zo! Zo wurin likita. Hehehe! Mene? Kai! Daina yi min magana! Kar ka matso kusa da ni! Hehehe! ...

**Mai gadi:** Ke mahaukaciyar yarinyar nan! Tashi daga wurin nan! Kina ba kwastomominmu tsoro. Tashi na ce! Dariya kike yi min? Kina ganin abin dariya ne? Na ce mi ki tashi ki bar wurin nan, in ba haka ba kuma in yi ƙwallo da ke!

**Amina:** Kai ne maras lafiya! Ni ce likitan!

**Mai gadi:** Shi ke nan! Na gaji da wannan shirmen naki. Bari ki gani!

**Amina:** Ka sake ni! Zan cije ka!

**Mai gadi:** Arrrrgh, shegiyar mahaukaciya! Kar ki ƙara zuwa nan wurin. In ba haka ba kuma sai na riƙa dukan mahaukacin kan nan naki har sai hankalinki ya dawo!

**Mai ba da labari:**

Yanzu bari mu bar kan titin, bari mu koma ƙauyen nan da aka ƙona gidan jinkan Duduwa. Kaddara dai ta sa ashe Duduwa ba ta cikin gidan lokacin da aka ƙona shi, lokacin ta je neman itace a daji. Bari mu iske ta a kan hanyarta ta komawa gida.

## Fitowa ta 4: A gidan Duduwa

**Duduwa:** Wayyo ɗana! Wayyo Musa! … Alhamdu lillahi, Musa! Allah na gode maka! Ba abin da ya same ka, ko Musa?

**Musa:** Zafi … zafi … Mama … zafi …

**Duduwa:** Na sani, Musa, yanzu ba wani abu. Mama ta dawo gida. Musa, ka yi haƙuri. Mama ta dawo. Na sani ɗana. Komai zai yi daidai. Yanzu Mama ta dawo kuma ba za ta ƙara barinka kai kaɗai ba.

**Mai gabatarwa:**

Da haka kuma muka kawo ƙarshen shirin na wannan lokaci. To yanzu me zai faru da Duduwa da ɗanta Musa? Shin Amina za ta samu wani taimako kuwa a kan titi? Amsoshin waɗannan tambayoyi za su kasance a shirinmu na gaba. Amma kuna iya tuntuɓarmu a adireshinmu na yanar gizo domin sake sauraron wannan shirin: dw.de/lbe. Kazalika kuna iya haɗewa da mu a shafinmu na Facebook. Sai mun sadu a shiri na gaba. Ku huta lafiya.